## Bayani game da bada amincewa kan sha'anin jima'i

Bada amincewa na nufin yanke shawara don radin kai domin yi wani abu da ya danganci jima'i. Bada amincewa za ta iya kasancewa ta hanyar furtawa ko kuma wani aiki da zai bada haske game da amincewar mutum kan aikita wani abu da ya danganci jima'i. Yin shiru ko ƙin nuna tirjiya ba ya nufin bada amincewar mutum. Ma'anar bada amincewar mutum ba ta banbanta kan jinsin mutum da kuma yanayin rayuwarsa ta jima'i.

Amincewa da duk wani aiki na jima'i ko kuma wani abu na jima'i da aka amince a yi a baya ba wai ya na nufin amincewa da wasu abubuwa na daban da ke da nasaba da jima'i ba.

Ana buƙatar bada amincewa ko da kuwa wanda ke kokarin yin abun na buge sakamakon shan barasa ko kuma ƙwayoyin da ke saka maye.

Mutum zai iya bada amincewarsa daga baya kuma ya janye wanan amincewa da ya yi a kowanne lokaci.

Ba za a iya bada amincewa kan wani abu da ya danganci jima'i ba in har mutum ba shi da zarafin badawa, hakan ka iya faruwa idan mutum ba zai iya zabar ai wannan aiki da shi ko akasin haka ba. Gaza bada amincewa ka iya faruwa idan mutum ba ya cikin hayyacinsa ko kuma idan ya na bacci ko kuma ma idan mutum ba zai iya bada amincewar baki ɗaya ba. Idan mutum na buge sakamakon shan barasa ko ƙwayoyin da ke sa maye ko kuma wasu abubuwa da ke bugarwa ba zai iya bada amincewarsa ba komai matsayin buguwar da ya yi.

Ba za a iya bada amincewa ba in har aka tursasawa mutum ko aka firgta shi ko aka yi amfani da karfi ko barazana ko kuma cutarwa.

Idan aka janye amincewar da aka bada ko kuma ya kasance ba za a iya badawa ba to dole ne a dakatar da yin jima'i.

## Samun afuwa daga chajin mutum sakamakon amfani da ƙwaya ko barasa

Lafiya da tsaro na kowanne ɗalibi a cikin makaranta Rockland Community College abu ne mai muhimmancin gaske. RCC ta gano cewar ɗaliban da ke shan barasa ko ƙwayoyin da ke saka maye (da niyya ko akasin haka) kan gaza bada bayani kan haka musamman ma idan abin ya haɗa da tashin hankali ciki kuwa har da rikici na cikin gida da rigima tsakanin masoya ko cin zarafi ta hanyar lalata, saboda irin abinda ka iya biyo baya sakamakon abinda suka aikata. RCC na karfafawa ɗalibai gwiwa kan su sanar da jami'an makaranta kan duk wani abu da ya danganci rikici na gida da rigima tsakanin masoya da cin zarafi ta hanyar lalata. Wanda ya shaida faruwar abu kuma ya ke da kyakkyawar niyya ko kuma mutumin da ya zaɓi sanar da hukumomi kuma shi ma ya ke da kyakkyawar niyya, in ya zaɓi bada bayani game da rikici na gida ko rigama tsakanin masoya ko cin zarafi ta hanyar lalata ga RCC jami'an makaranta ko jami'an tsaro ba za su yi masa hukunci da dokokin RCC's wadda ke hukunta wanda suka sha barasa ko ƙwaoyoyin da ke saka maye da aka yi amfani da su a lokaci da ake rikici na gida ko rigima irin ta masoya ko cin zarafi ta hanyar lalata.

## Kudurin 'yanci na ɗalibai

Dukkan ɗalibai na da 'yanci na:

Kai rahoto ga jami'an tsaro na yanki ko kuma 'yan sanda na jiha;

Bada bayani game da rikici na gida ko fada tsakanin masoya ko cin zarafi ta hanyar lalata kuma dole a ɗauke su da muhimmaci;

Yanke hukunci kan bada bayani game da laifi da aka aikata ko saɓawa doka ko ma shiga a dama da su a harkokin shari'a ba tare da tursasawa daga hukumar makaranta ba;

Shiga a dama da su a tsarin na gaskiya da adalci da kuma bada wadataccen lokaci na yin sanarwa da ma dama ta a saurari mutum;

Kula da su cikin yanayi na girmamawa daga jami'an makaranta tare kuma da sumun tsarin kiwon lafiya da bada shawarwari nagartatattu a inda ake da su;

Su kasance ba a zargesu da yin ba daidai ba idan sun bada bayani game da waɗannan laifuku ko saɓa doka da aka yi ko kuma su yin wani abu na daban don gujewa aikata irin waɗannan laifuka ko saɓa doka;

Yin bayani game da lamarin ga wasu wakilan makaranta 'yan ƙalilan ba kuma tare da an sanya mutum sake maimaita bayanin da ya yi a baya kan wannan batu ba.

Samun kariya daga ramuwar gayya daga jami'an makaranta ko ɗalibi ko kuma wanda ake tuhuma ko wanda ke bada ba'asi ko abokansu ko dangi da makusantansu waɗanda ke ƙarƙashin ikon makarantar;

Samun dama akalla guda ta ɗaukaka ƙara;

Samun rakiyar wani mai bada shawara da mai bada ba'asi zai zaba da kansa wanda zai taimaka masa tare da ba shi shawara a lokacin shari'a ko lokacin taruka da sauraron ba'asi da makamantansu;

Cin moriyar 'yanci da mutum ke da shi da yin addininsa ba tare da yi masa katsalandan ba daga ɓangaren masu bincike ko harka ta shari'a ta wannan makaranta.

Kowa zai iya cin moriyar 'yanci ba tare da la'akari da launin fata ko ƙasar da ya fito ba ko addini ko shekaru ko yanayi na nakasa ko jinsi ko irin tsarin da mutum ya fuskata ta fuskar jima'a ko aure da akasin haka ko juna biyu ko tawaya da ke da nasaba da ƙwayoyin hallita ko matsayin mutum a gidan soja da matsayin mutumin da aka ci wa zarafi ta hanya lalata ko kuma wanda aka taɓa ɗaurewa ba tare da la'akari da ko an aikata wannan laifi ne cikin makaranta ba ko lokacin da mutum ke karatu a ƙasar waje.

Ka na da 'yanci na ka sanar da 'yan sanda na jami'a ko jami'an tsaro na makaranta ko 'yan sanda ke yankinku ko ma 'yan sanda na jiha, kazalika mutum zai iya zaɓar ya ƙi sanarwa; sanar da abinda ya faru ga makaranta; samun kariya daga makaranta saboda yiwuwar fuskantar ramuwa ta gayya sakamakon bada ba wata sanarwa; da kuma samun tallafi da ma kuɗaɗe daga makaranta.